

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Rayuwar Jiki: Rayuwa Bayan Tashin Matattu

Yesu ya mutu domin mu kasance tare da Allah har abada



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Yesu ya ɗandana mutuwa ta kowace fuska domin kowane mutum don mu sami rai ta kowace fuska. Jiya, mun yi maganar fanni na farko, wanda rayuwa ce ta ruhaniya. A yau, za mu dubi fanni na biyu, wanda shi ne rayuwa ta jiki. Wannan rayuwa tana zuwa a matakai biyu a jere. Na farko, muna da rai a jikunanmu a yanzu. Amma jikunanmu na mutuwa ne; don haka, na biyu, a lokacin tashin matattu, za a canza jikunanmu zuwa jikuna marasa mutuwa.

> "In kuwa Ruhun wanda ya tada Yesu daga matattu yana zaune a cikinku [wannan yana nufin 'yana zaune a zuciyarku a yanzu haka ba sai bayan tashi daga matattu ba], to, shi da ya tada Kristi Yesu daga matattu zai kuwa raya jikin nan naku mai mutuwa ta wurin Ruhunsa da yake zaune a zuciyarku." (Romawa 8:11)

Dukan mu muna da jiki mai mutuwa da kuma rai na tashin matattu. Jikin mai mutuwa ne, amma da rai na tashin matattu a cikinsa. Ba kawai yana aiki a cikinsa ba ne, amma yana bayyane a cikinsa. Idan wannan ayar ba ta na magana a kan warkarwa da kuma ƙarfin jiki da kuzari na Allah ba, to, ban fahimci waɗannan kalmomi ba! Amma ba wannan ne ƙarshen ba. Karshen shi ne jikin da za a canza. Game da wannan jikin da za a canza, Bulus ya rubuta:

> "Ga shi, zan sanar da ku wani asiri! Ba dukanmu ne za mu yi barci ba, amma dukan mu za a canza kamanninmu; farat ɗaya da ƙyiftawar ido, da jin busar ƙaho na ƙarshe. Domin za a busa ƙaho, za a kuma ta da matattu da rashin ruɓa, za a kuma sauya kamanninmu. Domin lalle ne marar ruɓa ya maye mai ruɓar nan, marar mutuwa kuma ya maye mai mutuwa." (1 Korintiyawa 15:51–54)

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa tun da Yesu ya ɗandana mutuwa domina, ina da rai—

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

rai na tashin matattu a yanzu da kuma rai madawwami. Ina furta cewa Yesu ya mutu domin in saɗu da Allah har abada. Amin.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-149-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources

